

# TAIMAKO DAGA SAMA

MAI WA 'AZI —
WATSON GOODMAN

KYAUTA—KADA A SAYAR

## TAIMAKO DAGA SAMA

'TAIMAKO DAGA SAMA' An gyara shi kanana ne don ka yi anfani da shi lokacin da kana jiran wani kokuwa a kan tafiya. Kada ka battadda wannan lokaci; amma ka bada abinci ma ruhunka.

Na yi kokari in mai da rubutu babba da kuma saukin karatu. An debo kan magana daga wurare dabban dabban daga Litafi Mai Tsarki don na ba da gaskiya Litafi Mai Tsarkine yafi duka. Ina zato za mu fahinta Maganar Allah wanda ya ba mu a Litafi Mai Tsarki.

Kalman Allah ya sauko daga sama da kuma zai taimake zuciyar wanda ya karbe shi. In mutum ya tuba ya bar zunubi; ya bada gaskiya ga Mai Ceto; Yesu Almasihu, da dukan zuciyar shi, Allah zai ba shi murna da kwanciyar rai. Na gane ma'anar wannan a 1937, da dukan shekarun da suka biyo na sani ina tare da Ubangiji. Ina rokonka ka karbe Shi yanzu, in ba ka rigaya ba karbe shi ba. —Watson Goodman(1920-2002)



**Irmiya 31:3**

Ubangiji ya bayana gareni tun daga nesa, ya ce, Hakika, na yi ƙamnarka da madawamiyar ƙamna; domin wannan na jawo ka da rahama.

**Romawa 5:8**

Amma kuwa Allah na tabbatar mana da ƙaunad da ya ke mana, wato, tun muna masu zunubi, Almasihu ya mutu domimmu.

**Wahayin Yohana 1:5**

Da kuma Yesu Almasihu amintaccen mashaidi, Na Farko cikin masu tashi daga matattu, kuma mai mulkin sarakunan duniya. Ɗaukaka da mulki su tabbata har abada abadin ga wannan da ke ƙaunarmu, ya kuma ɓalle mana ƙangin zunubammu ta jininsa.

**Yohana 13:1**

Ana nan tun kafin Idin Ketarewa, da Yesu ya san lokacinsa ya yi da zai tashi daga wannan duniya ya koma wurin Uba, da ya ke ya ƙaunaci mutanensa da ke duniya, sai ya ƙaunace su har matuƙa.

**Yohana 3:16**

"Saboda ƙaunad da Allah ya yi wa duniya har ya ba da makaɗaicin Ɗansa, don duk wanda ya gaskata da shi kada ya halaka, sai dai ya sami rai madawwami."



An yi wannan ne duk don a cika abin da Ubangiji ya faɗa ta bakin annabin, cewa, "Ga shi, budurwa za ta yi juna biyu, ta haifi ɗa, Kuma za a sa masa suna Immanu'el." (Ma'anar Immanu'el kuwa, Allah na tare da mu.) —Matiyu 1:22, 23

**Yohana 1:1 da 14**

Tun fil'azal akwai Kalma, Kalman nan kuwa tare da Allah ya ke, Kalman nan kuwa Allah ne. . . . Kalman nan kuwa ya zama mutun, ya zauna a cikimmu, yana mai matuƙar alheri da gaskiya. Mun kuma dubi ɗaukakarsa, ɗaukaka ce ta makaɗaicin Ɗa daga wurin Ubansa.

**Yohana 14:9-10a**

Yesu ya ce masa, "Na daɗe tare da ku haka, amma har yanzu ba ka san ni ba Filibus? Duk wanda ya gan ni, ai ya ga Uban. Yaya, za ka ce, 'Nuna mana Uban'? Wato ba ka gaskata ba cewa ni cikin Uba na ke, Uba kuma cikina?

**1 Timotawas 3:16**

Babu shakka, asirin addinimmu muhimmi ne ƙwarai: Am bayyana shi da jiki, Ruhun ya nuna shi mai adalci ne, Mala'iku sun gan shi, An yi wa al'ummai wa'azinsa, An gaskata da shi a duniya, An ɗauke shi sama wurin ɗaukaka.



**Matiyu 3:17**

Sai aka ji wata murya daga sama ta ce, "Wannan shi ne Ɗana ƙaunataccena, wanda na ke farin ciki da shi ƙwarai."

**Kolosiyawa 2:9**

Don a cikinsa ne cikin jiki dukkan cikar allahntaka ke tabbata.

**1 Yohana 4:15**

Kowa ya bayyana cewa Yesu Ɗan Allah ne, sai Allah yă dawwama cikinsa, shi kuma a cikin Allah.

**Ishaya 9:6**

Gama an haifa mana yaro, a garemu an bada ɗa: mulkin za ya kasance a kafaɗassa: za a che da sunansa Al'ajibi, Maishawara, Allah mai-iko duka, Uba Madawami, Sarkin Salama.

**Luka 1:35**

Mala'ikan ya amsa mata ya ce, "Ruhu Mai Tsarki zai sauko miki, Ikon Maɗaukaki kuma zai lulluɓe ki. Saboda haka Mai Tsarkin nan da za a haifa za a kira shi Ɗan Allah."

**Matiyu 17:5**

Yana cikin magana sai ga wani gajimare mai haske ya zo ya rufe su. Aka kuma ji wata murya daga cikin gajimaren, ta ce, "Wannan shi ne Ɗana ƙaunataccena, wanda na ke farin ciki da shi ƙwarai. Ku saurare shi."

Yohana 9:5
"Muddar ina duniya ni ne hasken duniya."

Yohana 8:23
Sai ya ce musu, "Ku daga ƙasa ku ke, ni kuwa daga sama na ke. Ku na duniyan nan ne, ni kuwa ba na duniyan nan ba ne."

Yohana 11:25
Yesu ya ce mata, "Ai ni ne tashin matattu, ni ne kuma rai. Wanda ya gaskata da ni, ko ya mutu zai rayu."

Yohana 6:35
Yesu ya ce musu, "Ni ne Gurasa mai ba da rai. Wanda ya zo gare ni ba zai ji yunwa ba har abada, wanda kuma ya gaskata da ni ba zai ƙara jin ƙishirwa ba har abada."

Yohana 13:13
"Kuna kirana Malan, kuma Ubangiji. Daidai ne kuwa, don haka na ke."

Yohana 8:58
Sai Yesu ya ce musu, "Lalle, hakika, ina gaya muku, tun ba a haifi Ibrahim ba, ni ne."

Yohana 10:7
Don haka Yesu ya sake ce da su, "Lalle, hakika, ina gaya muku, ni ne ƙofar tumakin."



Matiyu 20:30 da 34
Sai ga mutum biyu makafi zaune a bakin hanya. Da suka ji dai Yesu ne ke wucewa, sai suka ɗaga murya suka ce, "Ya Ubangiji, ka ji tausayimmu, ya Ɗan Dawuda!" . . . Don kuma tausayi, sai Yesu ya taɓa idanunsu, nan take suka sami gani, suka bi shi.

Matiyu 14:19-21
Sa'an nan ya umarci taron su zazzauna a kan ɗanyar ciyawa. Da ya ɗauki gurasa biyar ɗin da kifi biyun, sai ya ɗaga kai sama, ya yi wa Allah godiya, ya guttsttsura gurasar, ya yi ta ba almajiransa, almajiran kuma suna bai wa jama'a. Duka kuwa suka ci suka ƙoshi, har suka kwashe ragowar gutsattsarin, cike da kwando goma sha biyu. Waɗanda suka cin kuwa misalin maza dubu biyar ne, ban da mata da yara.

Luka 5:5, 6
Siman ya amsa masa ya ce, "Ya Maigida, dare farai muna wahala, ba mu kama komai ba, amma da ka yi magana zan saki tarunan." Da suka yi haka kuwa, sai suka kamo kifi jingim, har ma tarunansu suka fara kecewa.



Ibraniyawa 1:2
Allah . . . a amma a zamanin nan na ƙarshe sai ya yi mana magana ta wurin Ɗansa, wanda ya sanya magajin komai, wanda ta wurinsa ne kuma ya halicci duniya.

Romawa 14:9
Saboda haka ne musamman Almasihu ya mutu, ya sake rayuwa, wato don ya zama shi ne Ubangijin matattu da rayayyu duka.

Kolosiyawa 1:16
Don ta gare shi ne aka halicci dukkan komai, abubuwan da ke sama da abubuwan da ke ƙasa, masu ganuwa da marasa ganuwa, ko kursiyai, ko masu mulki, ko masarauta, ko masu iko, wato dukkan abubuwa an halicce su ne ta wurinsa, kuma shi ne makoma tasu.

Yohana 1:3
Dukan abubuwa sun kasance ta gare shi ne, ba kuma abin da ya kasance a cikin abubuwan da suka kasance sai ta game da shi.

Ayyukan Manzanni 2:36
"Don haka sai duk jama'ar Isra'ila su sakankance, cewa shi Yesun nan da kuka giciye, Allah ya sanya shi Ubangiji, kuma Almasihu."



Yohana 5:22
Uba ba ya hukunta kowa, sai dai yā danƙa dukkan hukunci a hannun Ɗan.

Romawa 14:10
To, kai me ya sa ka ke ganin laifin ɗanuwanka? Kai kuma, me ya sa ka ke raina ɗanuwanka? Ai dukkammu za mu tsaya a gaban gadon shari'ar Allah.

2 Timotawas 4:1
Na gama ka da Allah, da kuma Almasihu Yesu, wanda zai yi wa rayayyu da matattu shari'a, na kuma gargaɗe ka saboda bayyana tasa da kuma mulkinsa.

Matiyu 25:32
Za a tara dukkan al'ummai a gabansa, zai kuma ware su daban daban, kamar yadda makiyayi ke ware tumaki da awaki.

Ayyukan Manzanni 10:42
Ya kuma umarce mu mu yi wa mutane wa'azi, mu kuma tabbatar cewa shi ne wanda Allah ya sanya mai hukunta rayayyu da matattu.

Romawa 2:16
A wannan rana Allah zai yi wa 'yan'adam shari'a a kan asirансu, ta wurin Yesu Almasihu, bisa Bisharad da na ke wa'azinta.



Ibraniyawa 5:9
Kuma da ya kai ga kammala, sai ya zama tushen madawwamin ceto ga dukkan waɗanda su ke masa biyayya.

Ibraniyawa 7:25
Saboda haka yana iya ceton masu kusantowa ga Allah ta wurinsa, matuƙar ceto, tun da ya ke kullum a raye ya ke saboda yi musu addu'a.

Ayyukan Manzanni 4:12
"Babu kuma samun ceto ga wani. Don ba wani suna duk duniyan nan da aka bayar cikin mutane, wanda lalle ta wurinsa ne za mu sami ceto."

Yohana 10:9
"Ni ne ƙofar. Kowa ya shiga ta cikina zai sami ceto, ya kai ya kawo, ya kuma yi kiwo."

Yohana 14:6
Yesu ya ce masa, "Ni ne hanya, ni ne gaskiya, ni ne kuma rai. Ba mai zuwa wurin Uba sai ta wurina."

Yohana 8:24
"Shi ya sa na ce muku za ku mutu da zunubanku. Don im ba kun gaskata cewa ni ne shi ba, za ku mutu da zunubanku."



Gama Allah ne ya sa kuka zama na Almasihu Yesu, Allah ne kuma ya sanya Almasihu ya zama hikima a gare mu. Ta wurin Almasihu ne kuma muka sami adalci da tsarkakewa da fansa. — I Korintiyawa 1:30

Wanda ya ba da kansa domimmu, don ya fanso mu daga dukkan mugun aiki, ya kuma tsarkake jama'a su zama abin mulkinsa, masu himmar yin kyakkyawan aiki. —Titus 2:14

Wahayin Yohana 5:9
Suna rera sabuwar waƙa, suna cewa, "Macancanci ne kai ka ɗauki littafin nan, ka ɓamɓare hatimansa, Domin dā an kashe ka, kuma ka fanso wa Allah mutane ta jininka Daga ko wace kabila, da ko wane harshe, da ko wace jama'a, da ko wace al'umma."

Luka 19:10
"Don Ɗam Mutun ya zo ne musamman neman abin da ya ɓāta, yă cece shi kuma."

Kolosiyawa 1:12-14
Kuna gode wa Uba, wanda ya maishe mu mu isa samun rabo cikin gadon tsarkakan da ke cikin haske. Ya tsamo mu daga mulkin duhu, ya maishe mu ga mulkin ƙaunataccen Ɗansa, wanda ta gare shi ne muka sami fansa, wato gafarar zunubammu.

## 10 TSARKAKA A JININ YESU

**Afisawa 1:7**
Ta gare shi ne muka sami fansa albarkacin jininsa, wato yafewar laifuffukammu, bisa yalwar alherin Allah.

**1 Yohana 1:7**
In kuwa muna zaune a cikin haske kamar yadda shi ya ke cikin haske, muna tarayya da juna ke nan, kuma jinin Yesu Ɗansa na tsarkake mu daga dukkan zunubi.

**1 Bitrus 1:18, 19**
Don kun san am fanshe ku ne daga al'adunku na banza da wofi da kuka gada, ba da abubuwa masu lalacewa ba kamar azurfa da zinariya, sai dai da jinin nan mai daraja na Almasihu, kamar na ɗan rago marar naƙasa, marar tabo.

**Ibraniyawa 9:14**
Balle fa jinin Almasihu wanda ya miƙa kansa marar aibu ga Allah, ta Madawwamin Ruhu, lalle zai tsarkake lamirimmu daga barin ibada maras tasiri, domin mu bauta wa Allah Rayayye.

**Romawa 5:9**
To, tun da ya ke yanzu an kuɓutad da mu ta jininsa, ashe kuwa ta wurinsa za mu fi samun karewa daga fushin Allah ke nan.

## CETO A WAJEN BANGASKIYA GA YESU KRISTI 11

**Afisawa 2:8, 9**
Don ta alheri ne aka cece ku saboda bangaskiya; wannan kuwa ba ƙoƙarin kanku ba ne, baiwa ce ta Allah, ba kuwa saboda aikin lada ba, kada wani ya yi alfahari.

**Romawa 5:1**
To, da ya ke mu kuɓutattu ne ta wurin bangaskiya, muna da salama ke nan a gun Allah ta wurin Ubangijimmu Yesu Almasihu.

**Galatiyawa 5:6**
In muna cikin Almasihu Yesu, kaciya da rashin kaciya ba a bakin komai su ke ba. Bangaskiya mai aikata ƙauna ita ce wani abu.

**1 Yohana 5:4**
Don duk wanda ke haifaffen Allah yana nasara da duniya. Bangaskiyarmu kuwa ita ce ta sa muka yi nasara da duniya.

**Yohana 20:31**
Amma an rubuta waɗannan ne, don ku ba da gaskiya Yesu shi ne Almasihu, Ɗan Allah, ta gaskatawa kuma ku sami rai a cikin sunansa.

**Yohana 6:28, 29**
Sai suka ce masa, "Me za mu yi mu aikata ayyukan da Allah ke so?" Yesu ya amsa musu ya ce, "Wannan shi ne aikin da Allah ke so, wato ku gaskata da wanda ya aiko."

## 12 TAUSAYIN ALLAH

**Zabura 103:11**
Gama kamar yadda sama ta yi nisa birbishin duniya, hakanan kuma jinƙansa yana da girma zuwa ga masu-tsoronsa.

**Zabura 103:17**
Amma jinƙan Ubangiji tun adun adun ne har abada bisa masu tsoronsa, adilcinsa kuma zuwa yayan yaya.

**Mikah 7:18**
Wanene Allah makwatancinka, mai gafarta mugunta, wanda ya rufe laifi na ringin mutanen gādonsa? ba ya riƙe fushinsa har abada ba, domin yana jin daɗin jinƙai.

**Zabura 108:4**
Gama jinƙanka yana da girma ya wuche sammai, gaskiyarka kuma ta kai har ga sararin sama.

**Makoki 3:22, 23**
Ta wurin jinƙan Ubangiji ba mun hallaka ba, gama rahamarsa ba ta sarewa. Sabuwa ce kowace safiya; amincinka da girma ya ke.

**Titus 3:5**
Sai ya cece mu, ba wai don wani aikin adalci da mu muka yi ba, a'a, sai dai don jinƙan nan nasa, albarkacin wankan nan na sake haifuwa, da kuma sabuntawan nan ta Ruhu Mai Tsarki.

## ALLAH YA CE MU ZO WAJEN SHI 13

**Matiyu 11:28**
Ku zo gare ni dukkanku masu wahala, masu fama da kaya, ni kuwa zan hutasshe ku.

**Wahayin Yohana 22:17**
Ruhu da Amarya suna cewa, "Zo." Duk wanda ya ji kuwa, yă ce, "Zo." Duk mai jin ƙishirwa ya zo, duk mai bukata yă ɗebi ruwan rai kyauta.

**Ishaya 55:1**
Ya ko, ɗowane dayanku mai jin ƙishi, ku zo wurin ruwaye, har da shi wanda ba shi da kuɗi; ku zo, ku saya, ku ci; i, ku zo, ku sayi ruwan anab da madara, ba da kuɗi, ba da abin biya ba.

**Yohana 7:37**
A ranar ƙarshe ta Idin, wato babbar ranar, sai Yesu ya tsaya, ya ɗaga murya ya ce, "Duk mai jin ƙishin ruwa yă zo gare ni yă sha."

**Ishaya 1:18**
Mu zo yanzu, mu yi binchike tare, in ji Ubangiji: ko da zunubanku sun yi kamar mulufi, za su yi fari kamar kankara snow: ko da suna ja wur kamar galura, za su zama kamar auduga.

## 14 BA DUKAN MUTANE NE 'YA'YAN ALLAH BA

**1 Yohana 3:10**
Ta haka sai a ga waɗanda ke 'ya'yan Allah, da kuma waɗanda ke 'ya'yan Iblis, wato duk wanda ba ya aikata adalci, ba na Allah ba ne, haka kuma wanda ba ya ƙaunar ɗanuwansa.

**Romawa 8:14, 15**
Duk waɗanda Ruhun Allah ke bishe su, su ne 'ya'yan Allah. Ai ruhun da kuka samu ba na bauta ba ne, har da za ku koma zaman tsoro. A'a, na zama 'ya'ya ne, har muna kira, "Ya Abba! Uba!"

**Filibiyawa 2:15**
Don ku zama marasa abin zargi, sahihai, 'ya'yan Allah marasa aibu a cikin zamanin mutane karkatattu, kangararru, waɗanda ku ke haskakawa a cikinsu kamar fitilu a duniya.

**2 Korintiyawa 6:17, 18**
"Saboda haka sai ku fito daga cikinsu, Ku keɓe, in ji Ubangiji. Kada ku ko taɓa wani abu marar tsarki; Ni kuwa in yi na'am da ku, In kasance Uba gare ku, Ku kuma ku kasance 'ya'yana, maza da mata, In ji Ubangiji Maɗaukaki."

**Yohana 1:12**
Amma duk iyakar waɗanda suka karɓe shi, wato masu gaskatawa da sunansa, ya ba su ikon zama 'ya'yan Allah.

## MAGANAR ALLAH A KAN SHA 15

**Ishaya 5:11**
Kaitonsu waɗanda ke tashi da sassafe domin su nemi barasa; masu rage dare, har ruwan anab ya buge su!

**Romawa 13:13, 14**
Mu tafiyadda al'amurammu yadda ya dace a yi da rana, ba cikin shashanci da buguwa, ko fasikanci da fajirci, ko jayayya da kishi ba. Amma ku ɗauki halin Ubangiji Yesu Almasihu, kada kuwa ku tanadi halin mutuntaka don biye wa muguwar sha'awa tasa.

**Galatiyawa 5:19-21**
Aikin halin mutuntaka a fili ya ke, wato, fasikanci, da aikin lalata, da fajirci, da bautar gumaka, da sihiri, da gaba, da jayayya, da kishi, da fushi, da sonkai, da tsaguwa, da hamayya, da hassada, da buguwa, da shashanci, da kuma sauran irinsu. Ina faɗakad da ku kamar yadda na faɗakadda ku a dā, cewa masu yin irin waɗannan abubuwa ba za su sami gādo a cikin Mulkin Allah ba.

**Misalai 23:31, 32**
Kada ka dubi ruwan anab sa'anda ya yi ja, Sa'anda yana bada launi cikin ƙoƙo, sa'anda yana gangarawa da daɗi: A karshe ya kan sare kamar machiji, ya kan yi harbi kamar kāsa.

## SAI KA BAYYAD DA KANKA DUKA

**Misalai 16:25**

Akwai wata hanya wadda ta ke da alamar kirki ga mutum, amma matuƙarta tafarkun mutuwa ce.

**Markus 10:17-22**

. . . "Malam managarci, me zan yi in gaji rai madawwami?" Sai Yesu ya ce masa, "Dom me ka kira ni managarci? Ai ba wani managarci sai Allah kaɗai. Ka dai san Umarnin nan: 'Kada ka yi kisankai, Kada ka yi zina, Kada ka yi sata, Kada ka yi shaidar zur, Kada ka yi zamba, Ka girmama mahaifinka da mahaifiyarka.' " Sai ya ce masa, "Malan, ai duk na kiyaye waɗannan tun ƙuruciyata." Sai Yesu ya dube shi duban ƙauna, ya ce masa, "Abu guda ne kawai ya rage maka. Sai ka je, ka sai da duk mallakarka, ka ba gajiyayyu, sai ka sami wadata a sama. Sa'an nan ka zo ka bi ni." Da jin wannan magana sai gabansa ya faɗi, ya tafi yana mai baƙin ciki, don yana da arziki ƙwarai.

**Matiyu 22:37, 38**

Ya ce masa, "Ka ƙaunaci Ubangiji Allahnka da dukkan zuciyarka, da dukkan ranka, da dukkan hankalinka. Wannan shi ne babban umarni kuma na farko.."

## KADA A CUCE KA



**Galatiyawa 6:3**

Kowa ya zaci shi wani abu ne, alhali kuwa shi ba komai ba ne, ya ruɗi kansa ke nan.

**Yakubu 1:22**

Amma sai ku zama masu aikata maganar, ba masu ji kawai kuna yaudarar kanku ba.

**1 Korintiyawa 6:9, 10**

Ashe ba ku san cewa marasa adalci ba za su sami gado a cikin Mulkin Allah ba? Kada fa a yaudare ku! Ba wasu fasikai, ko matsafa, ko mazinata, ko masu luɗu da maɗugo, ko ɓarayi, ko makwaɗaita, ko mashaya, ko masu zagezage, ko mazambata, da za su sami gado a cikin Mulkin Allah.

**1 Yohana 3:7, 8a**

Ya ku 'ya'yana ƙanana, kada fa kowa ya ɓadda ku. Shi wanda ke aikata adalci, mai adalci ne, kamar yadda Almasihu mai adalci ne. Duk mai aikata zunubi, na Iblis ne, don tun farko Iblis mai aikata zunubi ne. . .

**Afisawa 5:6**

Kada wani ya hilace ku da maganar wofi, gama sabili da waɗannan zunubai ne fushin Allah ke sauka kan kangararru.



## ZUNUBI TA KAWO MUTUWA

**Romawa 8:6**

Kwallafa rai ga al'amuran halin mutuntaka ƙarkonsa mutuwa ne, ƙwallafa rai ga al'amuran Ruhu kuwa rai ne da salama.

**Yakubu 1:15**

Mugun buri kuma in ya yi ciki, sai ya kan haifi zunubi. Zunubi kuma in ya balaga, sai ya kan jawo mutuwa.

**Ezekiel 18:20**

Wanda ya yi zunubi, shi za ya mutu: Ɗan ba za ya ɗauki laifin ubansa ba, uban kuma ba za ya ɗauki na ɗan ba: adilchin adili bisa kansa ya ke, muguntar mugu kuma a kansa.

**Misalai 11:19**

Wanda ya lizimchi adilchi za ya kai ga rai: mai-bin mugunta kuma mutuwar kansa ya ke bi.

**Romawa 5:12**

To, kamar yadda zunubi ya shigo duniya ta dalilin mutun ɗaya, zunubi kuwa shi ya jawo mutuwa, ta haka mutuwa ta zama gado ga kowa, don kowa ya yi zunubi.

**Luka 15:32**

" 'Ai kuwa daidai ne a yi ta murna da farin ciki, don ɗanuwan nan naka dā ya mutu, yanzu kuwa ya komo; dā ya ɓata, amma yanzu an same shi.' "

## YESU YA RINJAYI MUTUWA



**Luka 7:14, 15a**

Sa'an nan ya matso, ya taɓa makarar, masu ɗaukan kuma suka tsaya cik. Sai Yesu ya ce, "Samari, na ce da kai tashi." Mamacin sai ya tashi zaune, ya fara magana.

**Yohana 11:43, 44**

Da ya faɗi haka sai ya ɗaga murya da ƙarfi ya ce, "Li'azaru, fito!" Sai mamacin ya fito, ƙafa da hannu a ɗaure da abin likkafani, fuska tasa kuma a naɗe da mayani. Yesu ya ce musu, "Ku kwance masa ya tafi."

**Yohana 10:17, 18**

"Don wannan Uba ke ƙaunata, domin ina ba da raina in ɗauko shi kuma. Ba mai karɓe mini rai, don kaina na ke ba da shi. Ina da ikon ba da shi, ina da ikon ɗauko shi kuma. Na karɓo wannan umarni ne daga wurin Ubana."

**Wahayin Yohana 1:18**

"Ni ne kuma Rayayye. Dā na mutu, amma ga shi yanzu ina raye har abada abadin, ina kuwa da mabuɗan mutuwa da kuma na Hades."

**1 Korintiyawa 15:25, 26**

Don kuwa lalle ne ya yi mulki, har sai ya take dukkan maƙiyansa. Magabciyar ƙarshe da za a shafe, ita ce mutuwa.



## DOKOKIN ALLAH

**Kubawar Shari'a 5:7-21**

Ba za ka yi waɗansu alloli ba sai ni.

Ba za ka yi ma kanka wata ƙirba, surar kowane irin abin da ke cikin sama daga bisa, ko abin da ke cikin duniya daga kasa, ko kuwa abin da ke cikin ruwa daga karƙashin ƙasa: ba za ka yi sujada garesu ba, ba kuwa za ka bauta masu ba: . . .

Ba za ka kāma sunan Ubangiji Allahnkaa banza ba; gama Ubangiji ba za ya kuɓutadda wanda yana kāma sunansaa banza ba.

Ka tsare ranar assabbaci, domin a kiyaye ta da tsarki, kamar yadda Ubangiji Allahnka ya umurce ka, Kwana shidda za ka yi aiki, ka kuwa gama dukan aikinka: amma rana ta bakwai assabbar ne ga Ubangijin Allahnka: . . .

Ka bada girma ga ubanka da uwarka, kamar yadda Ubangiji Allahnka ya umurce ka: . . .

Ba za ka yi kisankai ba.

Ba kuwa za ka yi zina ba.

Ba kuwa za ka yi sata ba.

Ba kuwa za ka yi shaidar zur bisa makusancinka ba.

Ba kwa za ka yi ƙyashin matar makusanchinka ba; ba kwa za ka yi ƙyashin gidan makusanchinka, ko gonatasa, ko bawansa, ko baiwatasa, ko sansa, ko jakinsa, ko kowane abin da ke na makusanchinka.

## BA ZA KA IYA BUYA DAGA ALLAH BA



**Misalai 15:3**

Idanun Ubangiji suna chikin kowane wuri, Suna tsaron miyagu da nagargaru.

**Luka 8:17**

"Ba abin da ke ɓoye da ba za a bayyana ba. Ba kuma asirin da ba zai tonu ya zama bayyananne ba."

**Zabura 139:8, 12**

Idan na hau zuwa cikin sama, kana can: idan na yi shimfiɗata cikin Lahira, ga ka a can kuma. . . . Ko dufu ma ba dufu ne gareka ba, amma dare yana haskakawa kamar rana: da dufu da haske gareka duk ɗaya ne.

**Ayuba 34:21, 22**

Gama idanunsa suna duban tafarkun mutane, yana kwa ganin dukan hanyoyinsa. Babu wani dufu, ko inuwar mutuwa, inda masu aika mugunta za su ɓuya.

**Irmiya 23:24**

Akwai mai ɓuya a cikin lolokai har da ba zan gan shi ba? in ji Ubangiji. Ban chika sama da duniya ba? in ji Ubangiji.

## MUGUN WAHALA GA WADANDA BA 'YA'YAN ALLAH BA NE

**2 Bitrus 3:7**

Ta maganar Allah ne kuma sama da ƙasa da ke nan yanzu aka tanada su ga wuta, ana ajiye da su har ya zuwa ranan nan da za a yi wa marasa bin Allah shari'a, a hallaka su.

**Matiyu 25:46**

"Waɗannan ne za su shiga madawwamiyar azaba, masu adalci kuwa rai madawwami."

**Matiyu 13:41, 42**

"Ɗam Mutun zai aiko mala'ikunsa, za su tattaro duk masu sa mutane laifi, da kuma duk masu yin mugun aiki, su fid da su daga Mulkinsa, su kuma jefa su cikin wuta mai ruruwa. Nan za su yi kuka da cizon haƙora."

**Zabura 9:17**

Miyagu za su koma Lahira, watau dukan al'ummai waɗanda sun manta Allah.

**Matiyu 18:8**

"In kuwa hannunka ko ƙafarka na sa ka laifi, to, yanke shi ka yar. Zai fiye maka ka shiga rai da dungu ko da gurguntaka, da a jefa ka madawwamiyar wuta da hannu biyu ko ƙafa biyu."

## SHARI'A NA ZUWA



**2 Bitrus 2:9**

Ashe kuwa Ubangiji ya san yadda zai kuɓutad da masu tsoronsa daga gwaje-gwaje, ya kuma tsare marasa adalci kan jiran hukunci har ya zuwa Ranar Shari'a.

**1 Yohana 4:17**

Ta haka ne ƙauna ta cika a gare mu, har mu kasance da amincewa a Ranar Shari'a, domin kamar yadda ya ke, haka mu ma mu ke a duniyan nan.

**Ibraniyawa 9:27**

Kuma tun da ya ke an ƙaddara wa ɗan'adan ya mutu sau ɗaya ne, bayan haka kuma sai shari'a.

**2 Korintiyawa 5:10**

Don lalle ne a gabatad da mu duka a gaban gadon shari'ar Almasihu, don kowa ya sami sakamakon abin da ya yi tun yana tare da wannan jiki, ko mai kyau ko marar kyau.

**Romawa 14:12**

Don haka ko wannemmu zai faɗi abin da shi da kansa ya yi, a gaban Allah.

**Ayyukan Manzanni 17:31**

"Tun da ya ke ya tsai da ranad da zai yi wa duniya shari'a, shari'ar adalci, ta wurin mutumin nan da ya sanya, wannan kuwa ya tabbatar wa da dukan mutane, da ya tashe shi daga matattu."



## KAMNAR YESU KRISTI

**1 Bitrus 5:5b**

. . . "Allah na gāba da masu girman kai, amma yana yi wa masu tawali'u alheri."

**Ayyukan Manzanni 4:33**

Manzannin kuma suka yi shaida da tabbatarwa mai ƙarfi kan tashin Ubangiji Yesu daga matattu. Alheri mai yawa na tare da ko wannensu.

**Romawa 5:15**

Amma fa baiwan nan daban ta ke ƙwarai da laifin nan. Ai in laifin mutun ɗayan nan ya jawo wa masu ɗumbun yawa mutuwa, ashe ma alherin Allah, da kuma baiwan nan, albarkacin alherin Mutun ɗaya, Yesu Almasihu, sai su yalwata ga masu ɗumbun yawa fin haka ƙwarai.

**2 Korintiyawa 9:15**

Godiya tā tabbata ga Allah saboda baiwa tasa da ta fi gaban faɗi.

**2 Korintiyawa 8:9**

Domin kun san alherin Ubangijimmu Yesu Almasihu, ko da ya ke shi mawadaci ne, sai ya zama matalauci sabili da ku, domin ta wurin talaucinsa ku wadata.

**Romawa 9:16**

Ashe kuwa abin bai danganta ga nufin mutun ko himma tasa ba, sai dai ga jinƙan Allah.

## TUBA



**Matiyu 3:2**

Yana cewa, "Ku tuba, don Mulkin Sama ya kusato."

**Ayyukan Manzanni 17:30**

Dā kam Allah ya kau da kai ga zamanin jahilci, amma yanzu yana umartar dukkan mutane ko ina su tuba.

**Ayyukan Manzanni 3:19**

Saboda haka sai ku tuba, ku juyo, don a shafe zunubanku, Ubangiji kuma kansa ya riƙa wartsakad da ku.

**Ayyukan Manzanni 2:38**

Sai Bitrus ya ce da su, "Sai ku tuba, a yi wa ko wannenku babtisma, kan kun yarda da sunan Yesu Almasihu, don a gafarta zunubanku, za ku kuwa sami baiwar Ruhu Mai Tsarki."

**2 Korintiyawa 7:10**

Don baƙin ciki irin wanda Allah ke sawa shi ke biyarwa zuwa ga tuba, da kuma samun ceto, ba ya kuma sa "da na sani". Amma baƙin ciki kan al'amarin duniya shi ke jawo mutuwa.

**Luka 13:3**

Ina gaya muku, ba haka ba ne! In kuwa ba kun tuba ba, duk za ku halaka kamarsu.



## YAFEN ZUNUBAI

**Ishaya 55:7**

Mai-mugunta ya, săki hanyatasa, mara-adilci kuma ya bar tunaninsa; shi komo wurin Ubangiji, shi kuwa za ya jiƙansa; wurin Allahnmu, gama za ya yi gafara a yalwace.

**Ezekiel 18:21**

Amma idan mugu ya juya ga barin dukan zunubansa da ya aikata, ya kiyaye dukan farillaina, ya yi abinda ke halal da daidai kuma, hakika zai yi rai, ba zai mutu ba.

**Matiyu 6:14**

"Don in kun yafe wa mutane laifuffukansu, Ubanku na sama zai yafe muku."

**Wahayin 3:20**

" 'Ga ni nan tsaye a bakin ƙofa, ina ƙwanƙwasawa; kowa ya ji muryata ya buɗe ƙofar, sai in shiga wurinsa, in ci abinci tare da shi, shi ma kuma tare da ni.' "

**Ayyukan Manzanni 5:31**

"Shi ne Allah ya ɗaukaka ga hannun damansa, Shugaba kuma Maceci, don ya buɗe wa Isra'ila hanyar tuba, su kuma sami gafarar zunubansu."

**Markus 2:5**

Da Yesu ya ga bangaskiyarsu sai ya ce da shanyayyen, "Dana, an gafarta maka zunubanka."

## KU BA NA DUNIYA BA NE



**Afisawa 5:11**

Ku yi nesa da ayyukan duhu na banza da wofi, sai dai ku tona su.

**Ishaya 1:16**

Ku yi wanka, ku tsabtata; ku kawarda muguntar ayukanku daga gaban idanuna: ku bar yin mugunta.

**Titus 2:11, 12**

Alherin Allah ya bayyana saboda ceton dukkan mutane, yana koya mana mu ƙi rashin bin Allah da miyagun sha'awace-sha'awacen duniya, mu kuma yi zamammu a duniyan nan cikin natsuwa, da adalci, da kuma bin Allah.

**1 Yohana 2:15, 16**

Kada ku ƙaunaci duniya, ko abin da ke cikinta. Kowa ke ƙaunar duniya, ba ya ƙaunar Uba ke nan sam. Don kuwa duk abin da ke duniya, kamar su sha'awa irin ta halin mutuntaka, da sha'awar ido, da kuma alfarmar banza, ba na Uba ba ne, na duniya ne.

**Kolosiyawa 3:2**

Ku ƙwallafa ranku kan abubuwan da ke sama, ba kan abubuwan da ke ƙasa ba.

## SABUWAR HAIFUWA

**Ezekiel 36:26**
Sabuwar zuciya kuma zan ba ku, sabon ruhu kuma zan sa a cikinku: daga cikin jikinku kuma zan amshe zuciyan nan ta dutse, im ba ku zuciya mai-tabshi ta nama.

**1 Yohana 2:29**
Da ya ke kun san shi Mai adalci ne, ku dai tabbata cewa duk mai aikata adalci haifaffensa ne.

**1 Yohana 5:18**
Mun san cewa ko wane haifaffen Allah ba ya yin zunubi, kasancewarsa haifaffen Allah ita kan kare shi, Mugun nan kuwa ba ya taɓa shi.

**Yohana 3:3**
Yesu ya amsa masa ya ce, "Lalle, hakika, ina gaya maka, im ba an sake haifar mutum ba, ba zai iya ganin Mulkin Allah ba."

**1 Bitrus 1:23**
Gama sake haifarku aka yi, ba ta iri mai lalacewa ba, sai dai marar lalacewa, wato ta Maganar Allah rayayyiya, kuma dawwamammiya.

**2 Korintiyawa 5:17**
Saboda haka, duk wanda ke na Almasihu, sabuwar halitta ne, tsohon al'amari duk ya shuɗe, ga shi komai ya zama sabo.

## MUTUWA TA ZUNUBI: TASHI A YESU KRISTI



**Afisawa 2:1 da 6**
Ku kuma yā raya ku sa'ad da ku ke matattu ta laifuffukanku da zunubanku: . . . A cikin Almasihu Yesu kuma ya tashe mu tare har ya ba mu wurin zama tare a cikin samaniya.

**Kolosiyawa 3:1**
To, da ya ke an tashe ku tare da Almasihu, sai ku nemi abubuwan da ke sama, inda Almasihu ya ke, a zaune a hannun dama na Allah.

**1 Bitrus 2:24**
Shi da kansa ya ɗauki zunubammu a jikinsa a kan gungume, domin mu yi zamammu matattu ga zunubi, rayayyu ga adalci. Da raunukansa ne aka warkad da ku.

**Galatiyawa 5:24**
Waɗanda kuwa su ke su na Almasihu Yesu ne sun giciye halin mutuntaka da miyagun sha'awace-sha'awace iri iri.

**Romawa 6:2 da 11**
A'a, ko kusa! Mu da muka mutu ga zunubi, ƙaƙa za mu ƙara rayuwa a cikinsa har yanzu? . . . Haka ku ma sai ku lasafta kanku kan ku matattu ne ga zunubi, amma kuna raye, rayuwa ga Allah, ta Almasihu Yesu.



## RAI NA HAR ABADA

**Galatiyawa 6:8**
Wanda ya yi shuka a kwaɗayin son zuciyarsa, ta son zuciya zai girbi ruɓa. Wanda ya yi shuka a Ruhu, ta Ruhu zai girbi rai madawwami.

**Yohana 3:14, 15**
"Kamar yadda Musa ya ɗaga macijin nan a jeji, haka kuma dole ne a ɗaga Ɗam Mutun, don duk wanda ya gaskata da shi, ya sami rai madawwami."

**Yohana 3:36**
"Wanda ya gaskata da Ɗan, yana da rai madawwami. Wanda ya ƙi bin Ɗan kuwa, ba zai sami rai ba, sai dai fushin Allah ya tabbata a gare shi."

**Yohana 17:3**
"Rai madawwami kuwa shi ne, su san ka, Allah Makaɗaici na gaskiya, da kuma Yesu Almasihu da ka aiko."

**Yohana 5:24**
Lalle, hakika, ina gaya muku, duk mai jin maganata, ya ke kuma gaskata wanda ya aiko ni, yana da rai madawwami. Ba za a yi masa hukunci ba, don ya riga ya tsere wa mutuwa, ya kai ga rai.

**Romawa 6:23**
Gama sakamakon zunubi mutuwa ne, amma baiwar Allah ita ce rai madawwami cikin Almasihu Yesu Ubangijimmu.

## AKWAI CETO



**Ishaya 32:17**
Aikin adilci kuma salama ne: abin da adilci kuma za ya jawo sai kwanciyar rai da sakankanchewa har abada.

**Galatiyawa 4:6**
Tun da ya ke ku 'ya'ya ne, sai Allah ya aiko Ruhun Ɗansa cikin zukatammu, yana kira, "Ya Abba! Uba!"

**Yohana 14:21**
"Duk wanda ya san umarnina, ya ke kuma binsu, shi ne mai ƙaunata. Mai ƙaunata kuwa Ubana zai ƙaunace shi, ni kuma zan ƙaunace shi, im bayyana kaina gare shi."

**Romawa 8:16**
Ruhu kansa ma tare da namu ruhun suna yin shaida, cewa mu 'ya'yan Allah ne.

**1 Yohana 3:18, 19**
Ya ku 'ya'yana ƙanana, kada mu nuna ƙauna da fatar baki kawai, sai dai da aikatawa da kuma gaskiya. Ta haka za mu tabbata mu na gaskiya ne, har kuma mu amince wa kammu gaban Allah.

**1 Yohana 4:13**
Ta haka muka san muna dawwame cikinsa, shi kuma cikimmu, saboda Ruhunsa da ya ba mu.



## KRISTI YA KAN BADA MURNA

**Ishaya 12:3**
Domin wannan fa da murna za ku ɗiba ruwa daga rijiyoyi na cheto.

**Zabura 16:11**
Za ka bayana mani tafarkin rai: A gabanka akwai ƙoshin farinchiki; A cikin hannun damanka akwai jiyejiyen daɗi har abada.

**Yohana 15:11**
"Na gaya muku haka don farin cikina ya kasance a cikinku, farin cikinku kuma ya zama cikakke."

**Galatiyawa 2:20**
An giciye ni tare da Almasihu. Yanzu ba ni ne kuma ke raye ba, Almasihu ne ke raye a cikina. Rayuwan nan kuma da na ke yi ta jiki, rayuwa ce ta bangaskiya ga Ɗan Allah, wanda ya ƙaunace ni, har ya ba da kansa domina.

**Yohana 17:13**
"Amma yanzu ina zuwa wurinka. Ina faɗar wannan magana tun ina duniya don farin cikina ya zama cikakke a zukatansu."

**Romawa 14:17**
Ai Mulkin Allah ba ga al'amarin ci da sha ya ke ba, sai dai ga adalci da salama da farin ciki ta wurin Ruhu Mai Tsarki.

## TILAS KA BI MAI GIRMA



Ba ku sani ba, shi wanda ku ke miƙa kanku gare shi domin yi wa biyayya, lalle ku bayi ne na wanda ku ke yi wa biyayya ɗin (ko bautar zunubi wanda ƙarshensa mutuwa ne, ko bautar biyayya wadda ƙarshenta adalci ne)? — Romawa 6:16

**2 Tasalonikawa 1:7-9**
Ya kuma ba ku hutu har da mu ma, ku da a ke ƙuntata wa ɗin, a ranar bayyanar Ubangiji Yesu daga sama tare da manya-manyan mala'ikunsa, a cikin wuta mai ruruwa, yana ta saka wa waɗanda suka ƙi sanin Allah, da kuma waɗanda suka ƙi bin Bisharar Ubangijimmu Yesu. Za su sha hukuncin madawwamiyar halaka, suna ware da Zatin Ubangiji, da kuma maɗaukakin ikonsa.

**1 Samuila 12:15**
Amma idan kun ƙi saurara ga muryar Ubangiji, har kun tayas ma umurnin Ubangiji, sa'annan hannun Ubangiji za ya yi gāba da ku, kamar yadda ya yi da ubanninku.

**Kubawar Shari'a 11:26-28a**
Ga shi yau na sa albarka da la'ana a gabanku; idan kun kiyaye dokokin Ubangiji Allahnku, da na hukumta maku yau, albarka: amma idan kun ƙi dokokin Ubangiji Allahnku.

Filibiyawa 2:11
Ko wane harshe kuma yǎ yarda cewa Yesu Almasihu Ubangiji ne, don ɗaukaka Allah Uba.

Matiyu 10:32, 33
"Kowa ya bayyana yarda a gare ni a gaban mutane, ni ma zam bayyana yarda gare shi a gaban Ubana da ke cikin sama. Duk wanda kuwa ya yi musun sanina a gaban mutane, ni ma zan yi musun saninsa a gaban Ubana da ke cikin sama."

Romawa 10:9,10
Wato, in kai da bakinka ka bayyana yarda cewa Yesu Ubangiji ne, ka kuma gaskata a zuciyarka cewa Allah ya tashe shi daga matattu, za ka sami ceto. Don da zuci mutum ke gaskatawa yǎ sami adalcin Allah, da baki ya ke shaidawa ya sami ceto.

1 Yohana 2:23
Ba mai ƙin Ɗan ya sami Uban. Kowa ya bayyana yarda ga Ɗan, ya sami Uban ke nan.

Luka 9:26
"Duk wanda zai ji kunyar shaida ni da maganata, Ɗam Mutum ma sai ya ji kunyar shaida shi sa'ad da ya zo cikin ɗaukaka tasa, da kuma ɗaukakar Uba, da ta mala'iku tsarkaka."



2 Tasalonikawa 2:9
Mai tawayen nan kuwa zai zo ne bisa ikon Shaiɗan, yana aikata abubuwan al'ajabi, da alamomi, da aikin dabo na ƙarya iri iri.

1 Bitrus 5:8
Ku natsu, ku kuma zauna a faɗake. Magabcinku Iblis na zazzāgawa kamar zaki mai ruri, yana neman wanda zai lanƙwame.

Matiyu 4:1 da 10, 11
Sa'an nan sai Ruhu ya kai Yesu jeji domin Iblis yǎ gwada shi. . . . Sai Yesu ya ce masa, "Tafi daga nan kai Shaiɗan! don a rubuce ya ke, cewa, 'Kǎ yi wa Ubangiji Allahnka sujada, Shi kaɗai za ka bauta wa.' " Sa'an nan Iblis ya rabu da shi. Sai ga mala'iku sun zo suna yi masa hidima.

Afisawa 6:11
Ku yi ɗamara da dukkan makamai na Allah, don ku iya dage wa kissoshin Iblis.

Ayyukan Manzanni 26:18
" 'Don ka buɗe musu ido, su juyo daga duhu zuwa haske, daga kuma mulkin Shaiɗan zuwa wurin Allah, don su sami gafarar zunubai, da kuma gādo tare da dukan tsarkaka saboda sun gaskata da ni.' "



Yakubu 4:7, 8a
Saboda haka ku miƙa kanku ga Allah, ku yi tsayayya da Iblis, lalle kuwa zai guje ku. Ku kusanci Allah, shi ma zai kusance ku. Ku tsarkake al'amuranku, ya ku masu zunubi.

Ibraniyawa 2:14
Wato tun da ya ke 'ya'yan duk suna da tsoka da jini, shi ma sai ya ɗauki kamannin haka, domin ya hallakad da mai ikon mutuwa, wato Iblis, ta mutuwarsa.

Romawa 8:35 da 37
Wa zai iya raba mu da ƙaunadda Almasihu ke yi mana? Ƙunci ne? ko masifa? ko tsanani? ko yunwa? ko huntanci? ko haɗari? ko takobi? . . . Duk da haka kuwa a cikin wannan hali duka, har mun wuce ma a ce mana masu nasara, ta wurin wannan da ya ƙaunace mu.

1 Yohana 3:8
Duk mai aikata zunubi, na Iblis ne, don tun farko Iblis mai aikata zunubi ne. Dalilin bayyanar Ɗan Allah shi ne yǎ rushe aikin Iblis.

2 Tasalonikawa 2:8
Sa'an nan ne fa Sarkin tawayen zai bayyana, Ubangiji Yesu kuwa zai hallaka shi da hucin bakinsa, ya kuma shafe shi da bayyana tasa a ranar komowa tasa.



Kowa ya ce yana ƙaunar Allah, alhali kuwa yana ƙin ɗanuwansa, to, maƙaryaci ne. Don wanda ba ya ƙaunar ɗanuwansa da ya ke gani, ba dama ya ƙaunaci Allah wanda bai ma taɓa gani ba. — 1 Yohana 4:20

Galatiyawa 5:22, 23a
Albarkar Ruhu kuwa ita ce ƙauna, da farin ciki, da salama, da haƙuri, da kirki, da nagarta, da aminci, da tawali'u da kuma kamun kai.

1 Korintiyawa 13:1
Ko da zan yi magana da harsunan mutane, har da na mala'iku, amma ya zamana ba ni da ƙauna, na zama ƙararrawa mai yawan ƙara ke nan, ko kuge mai amo.

Yohana 21:16
Ya sake faɗa masa, faɗa ta biyu, "Siman ɗan Yohana, kana ƙaunata?" Ya ce masa, "I, ya Ubangiji, ka dai san ina sonka." Yesu ya ce masa, "Ka kiyaye tumakina."

1 Yohana 3:14
Mu kam mun san mun riga mun tsere wa mutuwa, mun kai ga rai saboda muna ƙaunar 'yanuwa. Wanda ba shi da kauna, zaman mutuwa ya ke yi.

"Ta haka kowa zai gane ku almajiraina ne, in dai kuna ƙaunar juna." — 1 Yohana 13:35



Da ya tashi da rai da wuri ranar farko ta mako, sai ya fara bayyana ga Maryamu Magadaliya, wadda ya fitar wa da aljannu bakwai. — Markus 16:9

Wanda aka bayar a kashe saboda laifofimmu, aka kuma tashe shi don mu sami kuɓuta ga Allah. — Romawa 4:25

Ayyukan Manzanni 10:39-41
Mu kuwa shaidu ne ga duk abin da ya yi a ƙasar Yahudawa da Urushalima. Shi ne kuma suka kashe ta kafe shi a jikin gungume. Shi ne Allah ya tasa a rana ta uku, ya kuma yarda ya bayyana, ba ga dukkan jama'a ba, sai dai ga shaidun nan da Allah ya zaɓa tun dā, wato mu ke nan, da muka ci muka sha tare da shi, bayan ya tashi daga matattu.

Yohana 20:26-28
Bayan kwana takwas har wa yau almajiransa na cikin gidan, Toma ma na nan tare da su, ƙofofi na kulle, sai ga Yesu ya zo ya tsaya a tsaka, ya ce, "Salamu alaikum." Sa'an nan ya ce da Toma, "Sa yatsanka nan, ka ji hannuwana. Miƙo hannunka kuma ka sa a kwiɓina. Kada ka zama marar ba da gaskiya, sai dai mai ba da gaskiya." Toma ya amsa masa ya ce, "Ya Ubangijina, kuma Allahna!"



Yohana 5:25 da 28, 29
"Lalle, hakika, ina gaya muku, lokaci na zuwa, har ma ya yi, da matattu za su ji muryar Ɗan Allah, masu ji kuwa su rayu. . . . Kada ku yi mamakin wannan, don lokaci na zuwa da duk waɗanda ke kaburbura za su ji murya tasa, su kuma fito, waɗanda suka aikata nagarta su tashi, tashin rai; waɗanda suka yi rashin gaskiya kuwa su tashi, tashin hukunci."

Romawa 6:3-5
Ashe ba ku san cewa duk ɗakwacin mu da aka yi wa babtisma cikin Almasihu Yesu, cikin mutuwa tasa aka yi mana babtismar ba? Saboda haka am binne mu da shi ke nan ta babtisma cikin mutuwa tasa, don kamar yadda aka ta da Almasihu daga matattu ta ɗaukakar Uba, haka mu ma mu yi zaman sabuwar rayuwa. Tun da ya ke mun zama ɗaya da shi wajen kwatancin mutuwa tasa, ashe kuwa za mu zama ɗaya ma wajen tashinsa.

Matiyu 16:21
Tun daga lokacin nan Yesu ya fara bayyana wa almajiransa lalle ne ya tafi Urushalima, ya sha wuya iri iri a hannun shugabanni da manyan firistoci da malaman Attaura, har a kashe shi, a rana ta uku kuma a tashe shi.

**1 Bitrus 1:15**

Amma da ya ke wanda ya kira ku mai tsarki ne, ku ma kanku sai ku zama tsarkaka cikin dukkan al'amuranku.

**Luka 1:74, 75**

Domin yana cetommu daga abokanan gabammu, Mu bauta masa ba da jin tsoro ba, Sai dai cikin tsarki da adalci a gabansa, Dukkan iyakar kwanakin nan namu.

**2 Korintiyawa 7:1**

Ya ku ƙaunatattu, tun da aka yi mana waɗannan alkawarai, sai mu tsarkake kammu daga ko wace irin ƙazanta ta jiki ko ta zuci, da bangirma ga Allah mu kamalta cikin tsarki.

**2 Timotowas 2:21**

Kowa ya tsarkake kansa daga ayyukan nan ƙasƙantattu, zai zama ma'aikaci mai daraja, tsarkakakke, mai amfani ga Ubangiji, shiryayye ga ko wane kyakkyawan aiki.

**1 Bitrus 1:2**

Su da ke zaɓaɓɓu bisa rigyasanin Allah Uba, waɗanda Ruhu kuma ya tsarkake, don su yi wa Yesu Almasihu Biyayya, su kuma tsarkaka da jininsa. Alheri da salama su yawaita a gare ku.



**Ibraniyawa 13:12**

Haka ma Yesu ya sha wuya a waje bayan birni, domin yă tsarkake jama'a da nasa jinin.

**1 Yohana 1:9**

In kuwa muka bayyana zunubammu, to, shi mai alkawari ne, kuma mai adalci ne, zai kuwa gafarta mana zunubammu, ya tsarkake mu daga dukkan rashin adalci.

**Ishaya 35:8**

A wurin kuwa za a taradda karabka da hanya kuma; za a ce da ita Hanyar tsarki; marasa-tsarki ba za su bi kanta ba; amma za ta kasance domin waɗannan; masu-tafiya, i, har marasa-wayo, ba za su ɓăta a ciki ba.

**Matiyu 3:11**

"Ni dai, da ruwa na ke muku babtisma shaidar tubanku, amma mai zuwa bayana ya fi ni girma, wanda ko takalmansa ma ban isa in riƙe ba. Shi ne zai yi muku babtisma da Ruhu Mai Tsarki, da kuma wuta."

**Afisawa 1:4**

Don kuwa ya zaɓe mu cikin Almasihu tun ba a halicci duniya ba, mu zama tsarkaka, marasa aibu a gabansa.



**Ayyukan Manzanni 1:8a**

Amma za ku sami iko sa'ad da Ruhu Mai Tsarki ya sauko muku, za ku kuma zama shaiduna. . .

**Ezekiel 36:27**

In sa ruhuna a cikinku, in biyadda ku cikin farillaina, za ku kiyaye shari'una, ku aikata.

**Romawa 8:9**

Amma ku kam ba masu zaman halin mutuntaka ba ne, masu zaman Ruhu ne, in dai har Ruhun Allah na zaune a zuciyarku. Duk wanda ba shi da Ruhun Almasihu kuwa, ba na Almasihu ba ne.

**Luka 11:13**

"To, ku da ku ke miyagu ma kuka san yadda za ku ba 'ya'yanku kyautar kyawawan abubuwa, balle Ubanku na sama da zai ba da Ruhu Mai Tsarki ga masu roƙonsa?"

**Ayyukan Manzanni 13:52**

Amma kuwa masu bi suna cikin farin ciki matuƙa, suna kuma cike da Ruhu Mai Tsarki.

**Ayyukan Manzanni 4:31**

Bayan sun yi addu'a, sai wurin da su ke tattare ya raurawa. Sai duk aka cika su da Ruhu Mai Tsarki, suka yi ta faɗar Maganar Allah gabagaɗi.



**Zabura 34:18**

Ubangiji yana kusa da masu-karyeyar zuciya, yana ceton irin waɗanda su ke da ruhu maituba.

**Ishaya 66:2**

Gama dukan waɗannan abu hannuna ya yi su, hakanan kuma dukan waɗannan abu sun faru da zamansu, in ji Ubangiji; amma da wannan mutum zan kula, shi wanda shi ke talaka mai-karyeyen ruhu, wanda ya ke rawan jiki da maganata.

**1 Bitrus 4:12, 13**

Ya ƙaunatattuna, kada ku yi mamakin matsananciyar wahalad da ta same ku kan gwaji, kamar wani baƙon abu ne ya ke faruwa gare ku. Amma muddar kuna tarayya da Almasihu wajen shan wuyarsa sai ku yi farin ciki, don sa'ad da aka bayyana ɗaukakarsa, ku yi farin ciki da murna matuƙa.

**Zabura 37:3**

Ka dogara ga Ubangiji, ka yi aikin nagarta; ka zamna a cikin ƙasan, ka lizamci aminci.

**Wahayin Yohana 21:4**

"Zai share musu dukkan hawaye. Ba kuma sauran mutuwa, ko baƙin ciki, ko kuka, ko azaba, don abubuwan dā sun wuce."



Allah Mai ba da salama kuwa zai sa ku tattake Shaiɗan da hanzari. Alherin Ubangijimmu Yesu Almasihu yă tabbata a gare ku. —Romawa 16:20

**Ibraniyawa 2:18**

Tun da ya ke shi ma ya sha wuya sa'ad da aka gwada shi, ashe zai iya taimakon waɗanda a ke wa gwaji.

**Ishaya 43:2**

Sa'anda ka ratsa ruwaye, zan yi tare da kai: sa'anda ka ratsa koguna kuma, ba za su dilmaye ka ba: sa'anda kana tafiya ta tsakiyar wuta, ba za ta ƙone ka ba; harshen wuta kuma ba za ya kama ka ba.

**Zabura 34:19**

Masifu na mai-adilci dayawa su ke: amma Ubangiji ya kan tsamadda shi daga chikinsu duka.

**Romawa 8:28**

Mun kuma san cewa al'amura duka na aikatawa tare zuwa alheri ga waɗanda ke ƙaunar Allah, wato waɗanda ke kirayayyu bisa nufinsa.

**1 Korintiyawa 10:13**

Ba wani gwajin da ya taɓa samunku, wanda ba a saba yi wa ɗan'adam ba. Allah mai alkawari ne, ba zai kuwa yarda a gwada ku fin ƙarfinku ba, amma game da gwajin sai ya ba da mafita, yadda za ku iya jure shi.



**Wahayin Yohana 3:5**

" 'Duk wanda ya ci nasara za a sa masa fararen tufafi, kuma ba zan soke sunansa daga Littafin Rai ba; zan ce shi nawa ne a gaban Ubana, kuma a gaban mala'ikunsa.' "

**Wahayin Yohana 2:7**

"Duk mai kunnen ji, yă ji abin da Ruhu ke faɗa wa ekiliziyai. Duk wanda ya ci nasara, zan ba shi izinin cin 'ya'yan bishiyar rai, wadda ke cikin Firdausin Allah.' "

**Wahayin Yohana 3:12**

" 'Duk wanda ya ci nasara, zan mai da shi ginshiƙi a haikalin Allahna. Ba zai ƙara fita daga ciki ba, zan kuma rubuta sunan Allahna a jikinsa, da sunan Birnin Allahna, wato Sabuwar Urushalima, mai saukowa daga wurin Allahna daga sama, da kuma nawa sabon sunan.' "

**Wahayin Yohana 21:7**

"Duk wanda ya ci nasara, zai ci wannan gado, wato in zama Allahnsa, shi kuma ya zama ɗa gare ni."

**Wahayin Yohana 3:21**

" 'Duk wanda ya ci nasara, zan ba shi izinin zama tare da ni a kursiyina, kamar yadda ni ma na ci nasara, na kuma zauna tare da Ubana a kursiyinsa.' "

**Matiyu 5:32**

"Amma ni ina gaya muku, kowa ya saki mata tasa, im ba a kan laifin zina ba, ya sa ta hanyar zina ke nan. Wanda kuma ya auri sakakkiya, ya yi zina."

**Luka 16:18**

"Kowa ya saki mata tasa ya auri wata, ya yi zina ke nan. Wanda ma ya auri sakakkiya ya yi zina."

**1 Korintiyawa 7:10, 11, 39**

Masu aure kuwa ina yi musu umarni, ba kuwa ni ba, Ubangiji ne, cewa, kada mace ta rabu da mijinta (in kuwa ta rabu da shi, sai ta zauna haka ba aure, ko kuwa ta sake shiryawa da mijinta); miji kuma kada ya saki mata tasa. . . . Igiyar aure na wuyan mace muddar mijinta na da rai. In kuwa mijinta ya mutu, tana da dama ta auri wanda ta ke so, amma fa sai mai bin Ubangiji.

**Romawa 7:2, 3**

Misali, mace mai aure shari'a ta ɗaure ta ga mijinta muddar yana da rai. Amma im mijinta ya mutu, ta kuɓuta daga igiyar auren ke nan. Don haka muddar mijinta na da rai, in ta auri wani, sai a kira ta mazinaciya. Amma im mijinta ya mutu, ta kuɓuta daga igiyar wannan auren.



**Yakubu 5:8**

Ku ma sai ku yi haƙuri, ku tsai da zukatanku, don ranar komowar Ubangiji ta yi kusa.

**Wahayin Yohana 3:11**

" 'Ina zuwa da wuri. Ka riƙi abin da ka ke da shi kankan, kada wani ya karɓe maka kambinka.' "

**Matiyu 24:27**

"Kamar yadda walƙiya ta ke wulgawa walai daga gabas zuwa yamma, haka komowar Ɗam Mutun za ta zama."

**Markus 8:38**

"Duk wanda zai ji kunyar shaida ni da maganata a wannan zamani na rashin amana da yawan zunubi, Ɗam Mutum ma sai ya ji kunyar shaida shi, sa'ad da ya zo cikin ɗaukakar Ubansa tare da mala'iku tsarkaka."

**Yohana 14:3**

"In kuwa na je na shirya muku wuri, sai in dawo in kai ku wurina, don inda na ke, ku ma ku zama kuna can."

**Matiyu 24:30**

A sa'an nan ne alamar Ɗam Mutun za ta bayyana a sararin sama, duk kabilun duniya kuma za su yi kuka, za su ga Ɗam Mutun na zuwa kan gajimare, da iko da ɗaukaka mai yawa."



**Wahayin 16:15**

"Ga ni nan tafe kamar ɓarawo! Albarka tā tabbata ga wanda ke zaune a faɗake, yana saye da tufafinsa, don kada ya tafi tsirara, a ga tsiraicinsa."

**Luka 12:40**

"Ku ma sai ku zauna a kan shiri, don a lokacin da ba ku zata ba Ɗam Mutun zai zo."

**1 Yohana 3:2**

Ya ku ƙaunatattuna, yanzu mu 'ya'yan Allah ne, yadda za mu zama nan gaba kuwa ba a bayyana ba tukuna, amma mun san cewa sa'ad da ya bayyana za mu zama kamarsa, don za mu gan shi kamar yadda ya ke.

**Matiyu 16:27**

"Don Ɗam Mutun zai zo cikin ɗaukakar Ubansa tare da mala'ikunsa. A sa'an nan ne zai sāka wa ko wane mutun gwargwadon aikinsa."

**Ayyukan Manzanni 1:11**

Sai suka ce, "Ya ku mutanen Galili, dom me ku ke tsaye kuna duban sama? Yesun nan da aka ɗauke daga gare ku aka kai shi sama, zai komo ne ta yadda kuka ga tafiyarsa sama."

**Luka 21:27**

"A sa'an nan ne za su ga Ɗam Mutun na zuwa cikin gajimare, da iko da ɗaukaka mai yawa."

## KALMAN ALLAH

Maganarka fitilla ce ga sawayena, haske ne kuma a tafarkina. –Zabura 119:105

Don ba wani annabcin da ya taɓa samuwa ta nufin mutun, sal dai mutane ne Ruhu Mai Tsarki ke izawa, Allah na magana ta bakinsu. –2 Bitrus 1:21

Na boye maganarka cikin zuchiyata, domin kada in yi maka zunubi. –Zabura 119:11

Don Maganar Allah rayayyiya ce, mai ƙarfin aiki, ta fi ko wane takobi kaifi, har tana ratsa rai da ruhu, da kuma gaɓoɓi har zuwā cikin ɓargo, tana kuma iya rarrabe tunanin zuciya da manufa tata. –Ibraniyawa 4:12

"Sararin sama da kasa za su shude, amma maganata ba za ta shuɗe ba." –Luka 21:33

Ko wane Nassi hurarre na Allah ne, mai amfani ne kuma wajen koyarwa, da tsawa tarwa, da gyaran hali, da kuma tarbiyyar aikin adalci. –2 Timotawas 3:16

Amma sai Yesu ya amsa musu ya ce, "Kun bàta ne, don ba ku san Littattafai ba, ba ku kuma san ikon Allah ba." –Matiyu 22:29

Published in numerous languages by World Missionary Press as God supplies funds in answer to prayer. If you would like more copies for careful distribution, write in English or visit **www.wmpress.org**.

**World Missionary Press, Inc.**
**P.O. Box 120**
**New Paris, IN 46553-0120 USA**

The New Testament Scripture text is from the New Testament in Hausa ©1972 by United Bible Societies Africa Regional Centre, Nairobi, Kenya. Used by permission.

27 Hausa HFA